

# Kudurorin Sabon Karn Na Majalisar Dunkin Duniya

# " Mu Jama'ar..."

A WAJEN TARON SABON KARNI
NEW YORK, 6 - 8 SATUMBA 2000

A Translation of "The Millennium Declaration"
Into Hausa

# Sashe na

# 1

## Kudurorin Sabon karni
## Na
## Majalisar Dunkin Duniya
## Rahoton Babban Sakatare

**Kofi Annan**
a wajen taron sabon karni
*New York, 6 - 8 Satumba 2000*

# Gabatarwa

Sanarwar sabon ƙarni wata takardar tarihi ce domin sabon ƙarni. An amince da ita a taron sabon ƙarni – da ya gabata daga 6 zuwa 8 na watan Satumba 2000 a birnin New York — yana ɗauke ne da damuwar da shuwagabannin ƙasashe 147 suka nuna, duk dai a ce tarsashin ƙasashe 191 ne suka halarci wannan taron da ya fi tara yawan shuwagabannin ƙasashe a Duniya.

Wannan sanarwar ta samu ne sanadiyyar tattaunawa da aka yi na watanni, da ba da ƙarfi da aka yi ga sauraren ra'ayoyin Nahiyoyi, da wani taron sabon ƙarnin da ya taimaka wajen sauraren koken jama'a. Na yi farin cikin ganin cewa yawancin alƙa wurra da ƙudurorin da na ba da shawara a cikin rahoton na sabon ƙarni yana cikin wannan sanarwar.

Niyyata ta shawarta yin wannan taro shi ne domini yin amfani da ƙarfin da wannan sabon ƙarni ya ke ɗauke da shi domin yayata bukatun da jama'a suke ɗauke da ita a ko'ina. Sauraren shuwagabanni da karatun sanarwar da suka amince da ita, na kaɗu akan irin ra'ayoyin da muke da su kan barazanar da muke fuskanta, da kuma irin kiran gaugawa da suka yi domin fuskantar barazanar.

Shuwagabannin sun aje lokacin da suke bukatar ganin sun rage yawan mutanen da ke fama da matsanancin talauci, samar da tsabtataccen ruwa da ilimi ga kowa, a rage yaɗuwar ciwon nan mai karya garkuwar jiki watau ƙanjamau (HIV/AIDS) da kuma cimma sauran manufofin ci-gaba. Sun kira ga faɗaɗa da ƙarfafa aikin kawo zawan lafiyar Majalisar Dunkin Duniya domin share hayawen raunana daga cikin al'ummu. Sun meme mu da mu yaƙi rashin adalci da nuna son kai, ba da tsoro da ta'addanci, kuma mù kare abin da muka yi tarayya akai, watau Duniya, domin al'ummu masu tasowa.

A cikin sanarwar, shuwagabannin Duniya sun bayar da ra'ayinsu na ganin cewa ƙungiyar ta dace da sabon ƙarni. Sun nuna suna son su ga majalisar Dunkin Duniya na da ta'asiri sosai. Suna son ta yi aiki da kuma samar da

kyakkyanwan sakamako. Ni dai a ɓangarena na sake sadaukar da kaina da ma'aikatana domin gudanar da wannan nauyi da aka ɗora mani. Amma dai abin tunawa a nan shi ne, su shuwagabannin nan sune majalisar Dunkin Duniya. Yana cikin huruminsu, don haka ɗawainiyarsu ce ganin sun cimma gacin manufofin da suka shata. Domin kansu, don ƙasashansu, da kuma mutanen Duniya baki ɗaya. Na ce: ku kaɗai ne ke da ƙarfin sanya majalisar Dunkin Duniya fuskantar ire-iren ƙalubalen da ke gabanta.

**Kofi A. Annan**
*Babban Sakataren majalisar Ɗunkin Duniya.*

*Babban taron majalisar Ɗunkin Duniya ya amince da waɗannan sanarwar:*

# Sanarwar majalisar Ɗunkin Duniya ta sabon ƙarni

## I. ABUBUWA MUHIMMAI DA AKIDOJI

1 Mu shuwagabannin ƙasashe da wakilansu, mun taru a hedikwatar majalisar Ɗunkin Duniya a birnin New York daga 6 zuwa 8 ga watan satumba 2000 a jijjihin sabon ƙarni, domin sabunta imanin da muke da shi akan majalisar Ɗunkin Duniya da Dokokinta a matsayin harsashen tabbatar da zaman lafiya, ci-gaba da adala a duniya.

2 Mun fashinci cewa bayan ɗawainiyar da muke da ita ta ƙasashenmu, mu na da wata ɗawainiyar baki ɗaya ita ce ta tabbatar da mutuncin bil'Adama, daidai to da adalci a duniya baki ɗaya. A matsayinwu na shuwagabannin mutanen Duniya ne, musamman masu rauni daga cikinsu, yaran duniya, da zasu zamo manya gobe.

3 Mun sabunta alƙawarinmu ga manufofi da aƙidojin Dokokin majalisar Ɗunkin Duniya, wanda ya dace da duk lokaci a ko'ina a cikin Duniya. Haƙiƙi muhimmancinsu dai ƙaruwa ya ke yi, domin irin dogaro da alakar ƙud-da-ƙud da ƙasashe da mutane a duniya suke da ita a yau.

4 Mun yi ƙudurin tabbatar da zaman lumana mai adalci a Duniya daidai da manufofi da dokokin majalisan Ɗunkin Duniya ya tanada. Mu na kara sadaukar da kanmu ga goyon bayan duk matakan da za'a ɗauka domin daidaita ƙasashe, mutunta iyakokinsu da 'yancinsu na siyasa, sasanta duk wani saɓani la lalama daidai da akidojin adalci da dokokin duniya, haƙƙi ne ga wuraren da suka saura ƙarƙashin mulkin mallaka na samun daman yin mulkin kansu, rashin yin shisshigi a cikin harkokin cikin

gidan wata ƙasa, mutunta dokokin haƙƙin Bi-Adama da Walwalarsu daidaita haƙƙoƙinsu ba tare da wariya ba na launin fata ko na jinsu (maza ko mata). harshe ko addini, da samun haɗin kan duniya wajen walwale wata matsala ta ƙasa da ƙasa da ta shafi tattalin arziki, mu'amala, al'ada ko abin da ya shafi halin Bil-Adama.

5 Mun yi imanin cewa ƙalubalen da mu ke fuskanta a yau shi ne tabbatar da samun nasarar shirin nan mai laƙabi da gulobalaizeshin (glovalization) ga al'ummar Duniya. Tun daɗewa gulobalaizeshin yana samar da abubuwan morewa masu yawa, amma a halin yanzu wasu wurare sun fi wasu morewa, haka nan kuma wasu wuraren sun fi wasu samunsa a cikin rahusa. Mun gano cewa ƙassshe masu tasowa da ƙasashen da tattalin arzikinsu ke cikin matsala sun fi sawun wahalar wannan shirin. Domin haka ne mu ke ganin samar da hanyar bai-ɗaya ta samun irin wannan shirin shi zai inganta mana rayuwa mai zuwa, daidai da matsayin Bil-Adama a duk fannonin rayuwarmu, ta haka ne shirin gulobalaizeshin zai samu nasara. Waɗannan matakan dole ne su haɗa da tsare-tsare da matakai a duniya na bai-ɗaya da ya dace da bukatun ƙasashe masu tasowa da tattalin arziki, haka a tabbatar da wajen aiwatar da shi sun taka rawa kyakkyawa.

6 Mun ɗauka cewa wasu abubuwa suna da daraja ko muhimmanci a cikin alaƙar ƙasa da ƙasa a cikin ƙarni naa shirin da ɗaya waɗanda suka haɗa da:

- **'Yanci:** Maza da mata suna da 'yancin rayuwa har su reni 'ya'yansu cikin mutunci, ba tare da barazanar yunwa ko ta'addanci ba, danniya ko rashin adalci. Demokuraɗiyyar da mutane suka amince da ita ce ta fi samar da waɗannan hakƙoƙin.
- **Daidaito:** Babu wani mutum ko ƙasa da za'a hana morewa daga abin da ci-gaba ya haifar. Dole ne a tabbatar da haƙƙoƙin bai-ɗaya tsakanin maza da mata.
- **Tallafawa:** Abaiban morewa na Duniya kamar (gulobalaizechin) dole ne a kula da hanyar samar da su ta bai-ɗaya, abin nufi a man shi ne sauƙi ko tsada

ya shafi kowa domin hakan ne ya fi **dacewa da dokar** adalci da sha'anin ma'amala. Masu samunsa da sauki sai su taimakawa masu samunsa da wahala.

- **Haƙuri da juna:** Dole Bil-Adama su mutunta junansu, duk da banbancin addininsu, al'ada da harsunansu. Banbanci a cikin al'unma ba abin tsoro ba ne idan aka yi yadda ya kamata. Ana bukatar samar da al'adar zama lafiya da tattaunawa domin bunƙasa lumana a cikin al'ummar duniya.
- **Mutunta albarkatu:** Ana son nuna ya kamata wajen ma'amala da abubuwa masu rayuwa da albarkatu, domin samun ci-gaba mai ɗorewa. Ta wannan hanyar ce kawai ɗinbin arzikin da Allah ya yi mana zai kai ga magadanmu. Halinmu na zari da al'mubazzaranci dole ne mu canza shi idan har mu na son al'ummar gaba da magada su more rayuwa.
- **Kowa Ma'aikaci ne:** Dawainiyar kula da tattalin arzikin duniya da jin-daɗin jama'a, da kawar da barazana ga zaman lumana da tsaro a duniya dole ne kowace ƙasa ta ba da na ta gudun-mawa a duniya. Ita kuma ƙungiyar nan da ta fi shahara da karɓuwa a Duniya watau majalisar Dunkin Duniya zata ba da matsayin heluma domin yin hakan.

7 Domin aiwatar da waɗannan manufofi, mun shata matakan da za'a bi don kai gaci.

## II. ZAMAN LAFIYA, TSARO DA KWANCE DAMARA

8 Za mu yi iyakan ƙoƙarinwu domin kare mutanenmu faɗawa cikin yaƙi, yaƙin basasa ne ko kuma na tsakanin ƙasa da ƙasa ne, yaƙi dai ya halaka rayukan fiye da mutane miliyan 5 a cikin shekarun da suka wuce. Har-ila-yau zamu yi ƙoƙarin kawar da barazanar da miyagun makamai suke yi.

9 Don haka nun yanke shawarar:

- Karfafa bin dokokin ƙasa da ƙasa kamar yadda ake bin dokar cikin gida, musamman za mu ƙarfafa bin

hukuncin da kotun daniya ta yanke ga ƙasashe a cikin shara'ar da ta shafe su daidai da tanadin da dokokin kundin majalisar Ɗunkin Duniya ya shata.

- Domin inganta ayyukan majalisar Ɗunkin Duniya wajen tabbatar da zaman lumana da tsaro ta hanyar samar da kuɗi da kayan aiki domin hana yaƙi, kwance ɗamarar yaƙi ta lallashi, kawo zaman lafiya, bayan ƙare yaki taimakawa wajen gina ƙasa da tabbatar zaman lafiya. A nan za mu yi la'akari da rahoton da kwamitin bincike da majalisar Ɗunkin Duniya ta kafa kan sha'anin ayyukan kawo zaman lafiyarta kuma za'a nemi Babban taron majalisar ya amince da shawarwarin yadda ya dace.
- Za'a ƙartafa haɗin kai tsakanin majalisar Ɗunkin Duniya da Kungiyoyin nahiyoyi, kamar yadda sashe na VIII na dokokin majalisar Ɗunkin Duniya ya yi tanadi.
- Don tabbatar da aiwatar da duk alkawurran da majalisar Ɗunkin Duniya ta yi, kamar su ƙayyade makamai, kwance ɗamarar yaƙi, dokokin duniya akan jin-ƙai da dokakin haƙin Bil-Adama, za'a yi kira ga duk ƙasashe su sanya hannu kuma su amince da dokokin duniya kan hana ta'addanci da aka tsara a birnin Rome.
- Za'a ɗauki ƙwaƙƙwaran mataki akan ta'addanci a duniya, kuma za'a gaggauta aiki da duk wasu alkawurran da aka ƙulla da suka shafi hanin ta'addanci.
- Za mu ninka ƙo-ƙarinmu na yaƙi da hana shan miyagun ƙwayoyi.
- Za mu ƙarfafa yaƙi da fataucin mutane da wanke haramataccin kuɗi zuwa kuɗin halas.
- Za'a ƙoƙarta ganin cewa takunkumin majalisar Ɗunkin Duniya bai yi ta'asiri sosai ba ga talakawa, za'a riƙa yin bitar takunkumin akai-akai domin tabbatar da cewa waɗanda basu ji basu gani ba basu wahala ba.
- Za'a ƙokarta domin kawar da miyagun makamai musamman mukaman Nukiliya, sannan zaa bar

ƙasashe su bi hanyoyin da suke ganin ya dace domin cimma wannan bukatar, haka za'a kira taron ƙarawa juna ilimi na Duniya don ƙara nemo hanyoyin kawar ɗa haɗarin makaman Nukiliya.

- Za'a ɗauki tsattasauran mataki akan halin nana na safarar ƙananan makamai, hanka duk inda za'a kai su ya kasance akwai masaniya. Za'a ƙarfafa ƙoƙarin Nahiyoyi na kwance ɗamarar yaki, tare da yin la'akari da shawarwarin taron ƙarawa juna ilimi na majalisar Dunkin Duniya da za'a yi kan sumogal ɗin ƙananan makamai don sayarwa a kasuwanin bayan fage.
- Za'a kira ƙasashe su yi aiki da tanadin da aka yi wajen taron nan na hana amfani da Nakiya, tare da, ƙera ta ko safaranta don samun daman ganin an lalata irin wannan makamin, har-ila-yau taron nan na hana amfani da nakiya da aka yi wa gyaran fuska za'a ƙarfafa amfani da shawarwarinsa.

10 Mu na kira ga ƙasasheda su goyi bayan ƙungiyar nan ta wasanni ta Duniya (Olympic) a matsayinsu na ɗaiɗaiku ko kuma a cikin ƙungiya, yanzu ko kuma a gaba, watau ƙoƙarin hada kan duniya ta hanyar wasanni da fahintar juna.

## III CI-GABA DA AYYUKAN KAWAR DA TALAUCI

11 Ba za mu yi kasala ba domin ganin mun fitar da maza, mata da yara a cikin mummunan halin da talauci ya jefa su, an ce akwai mutane fiye da biliyan da ke cikin wannan halin yanzu. Mun yi ƙudurin tabbatar da ayyukan ci-gaba ga kowa da fitar da jinsin Bil-Adama ga wata bukata.

12 Mun yanke shawarar samar da kyakkyawan muhalli — a cikin ƙasa da duniya baki ɗaya wanda ya dace da yanayin ayyukan ci-gaba da na kawar da talauci.

13 Samun cimma waɗannan biyan bukatun ya dogara ne ga samun kyakkyawar gwamnati da tsarin sha'anin

kuɗi da kawuwanci mai adala, mun yi ƙudurin samar da yanayi na kasuwanci da abin da ya shafi harkar kuɗi mai adalci da babu nunin bambanci a cikinsa ko son-kai.

14 Za mu himmantu da walwale matsalar da ƙasashe masu tasowa ke fama da ita watau ta rashin samun kuɗin ci-gaba da aikace-aikacen ci-gaba. Don haka za mu tabbatar da samun nasarar taron duniya da za'a yi kan samar da kuɗi ga 'yan kasuwa da gwammatoci domin aikace-aikacen ci-gaba, taron za'a yi shi ne 2001.

15 Haka mun yi ƙudurin taimakawa ƙasashen da basu ci-gaba ba. Don haka ne ma muke yin murna da zuwan taron majalisar Ɗunkiu Duniya na uku akan ƙasashen da basu ci-gaba ba da za'a yi a watan Mayu 2001 kuma za mu tabbatar da ganin nasarar taron. Don haka mu ke yin kira ga ƙasashe masu arzikin masana'antu su:

- A lokacin taron za'a amince da shirin nan na rashin sanyawa kayan da suka fito a ƙasashen da basu da cigaba kuɗin haraji;
- Zartar da shirin nan na yafe bashi ga ƙasashe talakawa da bashin ya yi wa tarnaƙi ba tare da ɓata lokaci ba, domin matalautan ƙasashen su kuma su saka da shirin nan na kawar da talauci a al'umma; da
- Ba da taimako afannin sha'anin ci-gaba ƙasashen da suke ƙoƙarin aiwatar da shirin nan na rage wa alumma talauci.

16 Mun kuma yi ƙudurin taimakawa ƙasashe talakawa da matsakaita da ke fama da matsalar bashi ta hanyar ƙara masu tsawon lokacin biyan basussukan nasu.

17 Mun kuma yi ƙudurin taimakawa shirin nan na musamman da aka yi ga tsibirai don aikace-aikacen ci-gabansu, ta aiwatar da shirin nan na Barbados da ya samu sakamakon zaman ashirin da biyu na Babban taron majalisar Ɗunkin Duniya. Hár-ila-yau mun kira al'ummar duniya da cewa su tabbata wajen zartar da shirin nan da aka yi domin tsibirai sun ba da ƙarfi don ci-gaban ƙananan tsibirai.

18 Mun fahimci bukatar musamman da ƙasashen nan da fadama ta kewaye, kuma mu na kira ga cibiyoyi masu ba da bashi da su ƙara yawan taimakon kuɗi da na ƙwararru ga ire-iren waɗannan ƙasashen domin su samu zartar da aikace-aikacen musamman na ci-gabansu, wannan zai taimake su kawar da matsalar yanayi da bunƙasa hanyoyin sufurinsu.

19 Har-ila-yau mun amince da:

- Rage yawan mutanen duniya da kuɗin shigarsu ya gaza dalar Amurka ɗaya a rana daga shekarar 2015, haka nan za mu rage yawan mutanen da ke fama da matsalar yunwa, cikin dai wannan shekarar ne mu ke son mu rage yawan mutanen duniya da basu da tsabtataccen ruwan sha.
- Za mu tabbatar cikin wannan watan, yara duk inda suke maza da mata sun sami kammala karatunsu na firamare, haka yaran maza da mata sun sami damar bai-ɗaya ta ci-gaba da karatunsu a manyan makarantu.
- A cikin dai wannan watan ne mu ke son rage curutan nan da ke kashe ƙananan yara da kashi uku cikin huɗu, haka su kuma yara 'yan shekara biyar za'a rage tasu curutan da kashi biyu cikin huɗu.
- A wannan lokacin ne ake son ganin an fara rage yaɗuwar ciwon nan mai kashe garkuwan jiki (HIV/AIDS), haka sannan ne ake son kyautata maganin zazzaɓin ciwon da dai duk sauran curuta da ke gallabar Bil-Adama.
- Samar da taimakon musamman ga yara da ciwon nan na ƙanjamau ya mayar marayu.
- A cikin shekarar 2020 ake son samun kyakkyawan ci-gaba ga rayuwar mutane aƙalla miliyan 100 da suke zaune a gidaje irin na talakawa kamar yadda shirin nan na inganta birane ya ba da shawara.

20 Mun yi ƙudurin:

- Karfafa daidaita jinsin maza da na mata da bunƙasa sha'anin mata a matsayin hanyar kawar da talauci, yunwa da curuta da ci-gaba mai ɗorewa.

- A bunƙasa ci-gaba da ɓullo da dabarar samar da aikin yi mai nagartaga matasa ko'in a cikin faɗin Duniya.
- Karfafa wa kamfanonin samar da magani gwiwa domin samar da magunguna masu inganci da arha duk inda ake bukatar su cikin ƙasashe masu tasowa.
- A yi haɗin gwiwa mai inganci tsakanin gwamnati da mutane masu zaman kansu domin samun ci-gaba mai dorewa da kawar da talauci.
- A tabbatar da cewa kowa na morewa sabin kafafen nan na watsa labarai ko sadarwa daidai da abin da taron ministoci ya ƙunsa wanda aka yi wa take da "ECOSOC 2000".

## IV KARIYAR MUHALLINMU

21 Ba za mu yi sake ba wajen kariyar Muhallinmu don amfanin Bil-Adama, haka za mu kare duniyarmu domin amfanin 'ya'yanmu da jikokinmu ka da su tashi cikin duniyar da harkokin Bil-Adama ya gurɓata, wadda albarkatun cikinta da zasu tarar ba zai isa gyara ta ba ballanta su biya ma kansu bukata.

22 Mun ƙarfafa goyon bayanmu ga aƙidar nan ta samun cigaba mai ɗorewa, da ta haɗa da abin nan da ke cikin lamba ta Zi da ke cikin taron ƙarawa juna ilima akan mahalli da cigabansa na majalisar Ɗunkin Duniya.

23 Mun amince cewa za mu ɗabbaƙar da duk shawarwarin da aka amince da su akan sha'anin muhallin da sabuwar hanya ta kariya ga muhalli, a matakin farko za mu:

- Tabbatar da fara aiki da bin da taron nan na birnin kyoto ya auince da shi mai take "kyo to protocel", amma kila zai iya kai lokacin bukin cika shekara goma da yin taron ƙarawa juna ilimi kan sha'anin muhalli da cigabansa a shekara 2002, haka za mu bukali rage zubar da sinadaran da ke illa ga tsiri mai take "greenhouse gases".
- Za mu ƙarfafa aikace-aikacenmu na kula da sha'anin

muhalli da ci-gaban sha'anin gandun daji.

- Za mu nemi a yi aiki da duk dokokin da ke da alaƙa da sha'anin muhlli domin hana gurgusowar hamada a cikin ƙasashen da ke fama da fari/ko hamada musamman a ƙasahen Afirka.
- A hana ɓarna ko ɓata ruwa ta hanyar ƙirƙiro hanyoyin samar da ruwa na za mani a tsakanin nahiyoyi, cikin ƙasa da ƙananan hukumomi domin samun ruwa tatacce kuma sasshe.
- Mu yi haɗin gwiwa don rage yawan raɗaɗin irin haɗarin da ake samu na mutane/ko kuma wanda Dollah ke kawowa.
- Mu tabbatar da samun bayani kyanta da sauƙi akan ilimin halittun Bil-Adama.

## V. HAKKIN BIL-ADAMA, DEMOKURADIYYA DA KYAKKYAWAN GWAMNATI (MULKI)

24 Za mu yi duk iyakan koƙarinmu domin bunƙasa demokuraɗiyya da shugabanci mai adalci, har-il-yau za mu ƙoƙarta ganin an mutunta duk abin da Duniya ta amince cewa 'yanci ne na Bil-Adama, haɗa da damar samun kafar ci-gaba.

25 Don haka mun yi kuɗurin:

- Za mu mutunta kuma za mu bi dokokin Duniya kan haƙƙin Bil-Adama.
- Za mu ƙokarta kayariya da bunƙasar da duk ƙasashe sha'nin mulkin farar hula, siyasa, tattalin arziki, Lamurran jin daɗin jama'a, da al'adu ga kowa.
- Faɗaɗa ra'ayi a cikin ƙasashenmu na zartar da mulkin demokuraɗiyya da aƙidojinta, da mutunta haƙƙoƙin Bil-Adama wanda ya haɗa da mutunta haƙƙin tsirarun ƙabilu.
- Za mu yaƙi duk wani nau'i na ta'addanci ga mata, kuma mu aiwatar da shawarwarin da aka amince da su a wajen taron nan na ƙara wa juna ilimi akan kawar da duk wani nau'in bambanci ga mata.

- Za mu ɗauki matakan tabbatar da an mutunta kuma a bunƙasa haƙƙoƙin Bil-Adama da ya shafi 'yan gudun hijira, ma'aikata 'yan gudun hijira da iyalansu, haka za mu kawar da bambancin launin fata da barazanarsa ke ƙaruwa a al'ummu da dama, domin bunƙasa haɗin kai da haƙuri da juna a cikin al'ummu.
- Za mu yi aiki baki ɗaya domin samun mulkin siyasa marasa nuna bambanci ga kowa, a baiwa 'yan ƙasa damn ba da gudun-mawarsu domin samun mulkin siyasa ingantacce a ƙasashe.
- Za mu tabbata cewa ma'aikatan watsa labarai sun samu cikakken 'yancin yin aiki, domin jama'a su sami damar samun ingantattun labaraci.

## VI KARIYA GA MASU RAUNI

26 Za mu ƙoƙarta ganin cewa yara da farar hular da wani bala'i ya faɗa masu, kisan ƙare dangi da yaƙi sun sami irin taimakon jin-ƙai da irin kariyar da ya kamata domin su koma yin rayuwa kamar kowa a cikin sauri.

Don haka mun yi ƙudurin:

- Faɗaɗa da ƙara kariya ga al'ummar farar hula don hana su shiga halin ƙaƙa-nika yi, kamar dai yadda dokokin Duniya kan haƙƙin Bil-Adama ya tanada.
- Faɗaɗa haɗin kan duniya da ya haɗa da raba ɗawainiya ta ganin kula da taimakawa ga sha'anin jin-ƙai ga ƙasashen da suka ɗauki baƙuntar 'yan gudun hijiran har su sami sararin komawa ƙasarsu cikin ra'ayin kansu cikin isasshen kariya da mutunci, har su fara rayuwarsu a cikin al'ummarsu. Kamar yadda suka saba.
- Karfafa ganin an aiwatar da dokokin duniya kan haKKin yara da ya hana saka yara aikin soje, ya hana sayar da su, da sa su karuwanci ko ɗaukar hotonsu tsirara.

## VII BIYAN BUKATAR AFIRKA TA MUSAMMAN

27 Za mu baiwa kiraye-kirayen neman demokuraɗiyya da'yan Afirka suke yi goyon baya, haka za mu taimaka masu domin ganin samun ingantaccen zaman lafiya, kawar da'talauci, da ci-gaba mai ɗorewa, domin ita ma Afirka ta shiga cikin sahun duniya wajen ƙarfin tattalin arziki.

28 Don haka mun yi ƙudurin:

- Goyon bayan siyasa da cibiyoyin neman demokuraɗiyya a Afirka.
- Za mu ƙarfafa kuma muga cin nasarar kafafen hana yaƙi a Nahiyoyi, za mu tabbata an sami ingantacciyar siyasa, haka za mu tabbata an sami kuɗin gudanar da ayyukan kawo zaman lafiya a Nahiya.
- Za mu ɗauki matakan musamman domin cin nasarar shirin kawar da talauci da samun ci-gaba mai ɗorewa a nahiyar Afirka, da ya haɗa da soke bashi, bunƙasa sha'anin kasuwanci mai sauƙi, taimakona gwaunatoci ga sha'anin ci-gaba, da neman 'yan ƙasashen waje zuba jari, da taimakawa a fannin fasaha.
- Za mu taimakawa Afirka hana yaɗuwar ciwon ƙanjamau da sauran curuta da wani ke iya ɗauka daga wani.

## VIII KARFAFA MAJALISAR ƊUNKIN DUNIYA

29 Za mu yi duk iyakan ƙoƙarinmu domin ganin cewa majalisar Ɗunkin Duniya ta samu irin ƙarfin da ta ke bukata wajen cimma waɗannan manufofin: gwagwarmayar samun ingantaccen ci-gaba a ko'ina cikin duniya; yaƙi da talauci; jahilci da curuta; yaƙi da rashin adalci; yaƙi da ta'addanci, zalunci da miyagun laifuka; da kuma yaki akan duk abin da zai ruguza ko lalata mana muhallinmu (Duniya).

30 Karfafa Babban taron majalisar Ɗunkin Duniya a matsayinsa na wuƙa da nama wajen tsara aikace-aikace da kuma Babban rashen da ke wakiltan majalisar Ɗunkin Duniya kuma za mu iyakan ƙoƙarinmu ganin ya yi wannan aikin da kyau.

- Za mu ƙoƙarta ganin an yi wa majalisar tsaro gyaran fuska a duk fannonin da suka dace.
- Za mu ƙarfafa majalisar tattalin arziki da jin-daɗi, domin taimaka mata ganin ta sauke nauyin da aka ɗora mata.
- Za mu ƙarfafa kotun Duniya domin tabbatar da adalci da bin doka a tafiyar da al'amurran duniya.
- Za mu ƙarfafa muhimmancin tuntuɓan juna tsakanin rassan majalisar Ɗunkin Duniya don gudanar da aikace-aikacensu yadda ya kamata.
- Za mu tabbata cewa ƙungiyar ta samu kuɗin da ta ke bukuta cikin lokaci, kuma a inda ake bukatar su domin zartar da ayyukanta.
- Za mu umurci Babban Sakatariya ta yi amfani da waɗannan kuɗaɗen akan abin da Babban taron majalisar Ɗunkin Duniya ya yanke shawara akai, daidai da ra'ayin 'yan wannan ƙungiyar, ta bin hanyoyin zamani kan sha'anin sarrafa abu da na fasaha kamar ɗai yadda ƙasashen da ke cikin ƙungiyar suka nuna sha'awar a yi.
- Za mu ƙarfafa bin shawarwarin taron nan akan sha'anin tsaro da kariya ga ma'aikatan majalisar Ɗunkin Duniya.
- Za mu tabbata cewa an samu cikakken haɗin kai tsakanin majalisar Ɗunkin Duniya, da rassanta, da cibiyoyin Bretton woods da ƙungiyar ciniki ta duniya kai da dai sauran ƙungiyoyin duniya domin haɗa kai wajen samun zaman lafiya da ci-gaba mai ɗorewa a Duniya.
- Za mu kuma ƙarfafa samun haɗin kai tsakanin majalisar Ɗunkin Duniya da majalisar Dokokin ƙasashen Duniya a ƙarƙashin ƙungiyarsu ta fannoni daban-daban da suka haɗa da: zaman lumana da

tsaro, tattalin arziki da ci-gaban jama'a, dokokin duniya da hakkin Bil-Adama, da sha'anin da ya shafi demokuradiyya da daidaita jinsi.

- A baiwa kamfanoni da kungiyoyi masu **zaman** kansu karin dama, da al'ummar farar hula su bayar da gudun-mawa domin ganin samun nasarar shirye-shirye da manufafin kungiyar.

31 Mu na yin kira ga Babban taron majalisar ya yi bita lokaci-lokaci domin ganin irin nasarar da aka samu wajen aiwatar da wadannan kudurorin, har-ila-yau su nemi shima Babban sakatare da ya ba da rahoton da Babban taro zai dora akan ginar da aka yi.

32. Mu na kara karfafa wa a wannan taro mai tarihi cewa majalisar Dunkin Duniya ita ce Kungiyar da ta hada duk mutanen duniya a matsayin iyalai daya, a karkashinta ne muke fatar samun biyan bukatarmu ta samun zaman lafiya, hadin kai da ci-gaba. Don haka mu na ba da cikakken goyon bayanmu ga wadannan kudurin da kuma kokarin cimma wannan manufar.

*Kudurorin A/RES/55/2*
*8 Satumba 2000*

# MU JAMA'AR

## MAJALISAR ƊUNKIN

## DUNIYA DA

## AIKACE-AIKACENMU

## *A CIKIN KARNI NA 21*

Rahoton da Babban Sakataren Majalisar Ɗunkin Duniya ya ba da ga ƙungiyar akan taron sabon ƙarni da majalisar ta yi.

A TAKAICE

2000

United Nations

Majalisar Ɗunkin Duniya




Mu Jama'ar Majalisar Ɗunkin Duniya da aikace-aikacenmu a cikin ƙarni na 21 mun gamsu da cewa zagayowan ƙarni wani abu ne na "musamman da ke tilasta mu buɗe sabon shafi domin yin aiki ga manufofin Majalisar Ɗunkin Duniya a cikin sabon shekara, Babban Taron Majalisar Ɗunkin Duniya ya amince a cikin watan Disamba 1998 cewa zai zayyana zamansa na 55 ya fara 5 ga watan Satumba 2000, a matsayin Taron Majalisar Ɗunkin Duniya na sabon ƙarni. Har-ila-yau taron ya amince da shirya taron ƙarawa juna ilimin da za'a yi a 6 zuwa 8 ga watan Satumba 2000.

A shirye-shiryen da ake yi domin ƙaddamar da taron ƙarawa juna ilimin, wanda ake zaton ya zama shi ne taro mafi girma da ya tara shugabannin ƙasashe da shugabannin gwamnatoci, Babban Sakataren Majalisar Ɗunkin Duniya, Kofi Annan ya ƙaddamar da rahotonsa na sabon ƙarni 3 ga watan Afirilu 2000. Rahoton na da take 'Mu Jama'ar: Aikace-aikacen Majalisar Ɗunkin Duniya a cikin ƙarni na 21". Ya bayyana matakan da za'a bi domin yin aiki ga al'umar duniya ko'ina suke. Shi ne bayanin da ya fi duk irin bayanan da aka taɓa yi a tsawon tarihin rayuwar ƙungiyar na shekaru hamsin da biyar da ya bayyana manufofin majalisar, rahoton ya ƙunshi manufofi da tsare-tsare waɗanda BabbanSakataren ke neman shuwagabannin ƙasashe su amince da shi. Sune nan aka taƙaita a ƙasa.

**Sabon Karni, Sabon Kalubole**

Sabon ƙarni da taron sabon ƙarni, suna ba mutanen duniya wata dama ta musamman don yi tunani kan makomarsu, a lokacin da suka sami kan su a harharɗe da juna irin harɗiyar da ba'a taɓa samun irinsa ba a da. Don haka suna sa ransu cewa shuwagabanninsu zasu gano irin Kalubalen da suke fama da shi su kuma yi masu magani. Majalisar Ɗunkin Duniya na iya taimakawa domin kawar da duk wata ƙalubale idan har duk mambobin ƙungiyar zasu sabonta ƙoƙarinsu don cin nasarar manufofin ƙungiyar. Ita dai ƙungiyar an ƙirƙiro ta ne a 1945 domin samar da alaƙa ingantacciya a tsakanin mutane a duniya. Ba shakka Majalisar Ɗunkin

Duniya ta samu nasara a wasu to fannoni fiye da wasu wuraren. Wannan wata dama ce da za'a sake yi wa Majalisar Ɗunkin Duniya kwaskwarima domin sama wa mutane ingantacciyar rayuwa a cikin sabon ƙarni.

**Cigaban Duniya da Sha'anin Mulki**

Amfanin ɗaubar Duniya tamkar ƙasa ɗaya abu ne wanda ya ke muraran: saurin cigaba, ingantacciyar hanyar rayuwa, da sabin hanyoyin more rayuwa. Duk da haka dai an fara samun tabo domin waɗannan hanyoyin more rayuwar ba'a yin raba dai-dai a cikin sha'aninsu, kuma abin da ya shafi sha'anin kasuwancin duniya bai samu dokar bu ɗaya ba da zata tabbatar da kowa na jin daɗin manufar.

A cikin shekarar 1945 waɗanda suka kafa wannan ƙungiyar sun shata buɗaɗɗiyar hanyar haɗin kan duniya ce baki ɗaya. Kuma wannan tsarin ya yi aiki, domin sanadinsa ne har aka samu ra'ayin cewa duniya kamar ƙasa ɗaya ce (*globalization*). A sakamakon haka yanzu muna zaune a duniya tamkar ƙasa ɗaya, kuma amsa wannan kira wata ƙalubale ce ga shuwagabannin duniya a yau.

A cikin wannan sabuwar duniyar, ƙungiyoyi da mutane sai ma'amala suke ta ƙara yi da juna a kai tsaye duk fannoni, ba tare da sa bakin ƙasashensu ba. Sabin hanyoyin fasaha suna samar da kafar ma'amala da fahimtar juna da kuma irin matakin bai-ɗaya da ya kamata a ɗauka kan wata matsala. Amma har-ila-yau akwai sabin haɗari da ake fuskanta. Miyagun laifuka, miyagun ƙwayoyi, ta'addanci, gurɓata muhalli, cututa, makamai, 'yan gudun hijira da masu yin hijira duk suna tafi kan iyakoki da sauri kuma da yawa fiye da lokacin da ya wuce. Mutane suna jin barazanar abubuwan da ke faru wa nesa da su. Kuma suna ƙara samun sanayyar rashin adalci da muguntar ƙasashe da ke nesa da su har suna sa ran ƙasashe su yi wani abu akan hakan. Idan muna son mu more zaman duniya a matsayinta na ƙasa ɗaya kuma mu guje wa duk wani mugun abu, to dole ne mu koyi yin kyakkyawan mulki, da yadda zamu yi mulki kyakkyawa a duniya baki ɗaya.

Wannan ba yana nufin gwamnatin duniya baki ɗaya ba ko kuma haɗe duk ƙasashe su zama ɗaya ba. A'a abin nufi shi ne ƙasashe da yawa na bukatar a ƙarfafa su, zasu iya samun ƙarfin da suke bukata daga junansu ta hanyar aikata abu bai-ɗaya a cikin ƙungiya da kowa zai bi daka irin ɗaya

da manufofi iri ɗaya . Waɗannan cibiyoyin dole ne su dace da lokaci. Kuma zasu iya zama tamkar wuraren da ƙasashe zasu yi aiki cikin haɗin gwiwa da waɗanda ba gwamnatoci ba da suka da kamfanoni. A wani lokaci ma ana son su ƙasashe su sami mataimaka ba lallai irin waɗanda aka zauna aka yi 'yarjejeniya da su a rubuce ba da zasu amsa kira nan take ga abin da duniya ta kira a aikata.

Gibin da ake samu a wajen mallakar dukiya a duniyarmu a yau, halin matsanancin talanci da mutane fiye da biliyan ɗaya suke ciki, yawaita samun miyagun yaƙe-yaƙe a nahiyoyi, da sauran lalata muhalli: duk wannan shi ne ya tattaru ya hana ɗorewar cigaban da aka samu a zamanin nan, sai fa idan an haɗu an ɗauki matakan bai ɗaya da zai hana hakan.

Wani binciken jin ra'ayin jama'a da aka gudanar ba da daɗewa ba a nahiyoyi shida na duniya—mafi girma da aka taɓa yi—ya tabbatar da cewa irin wannan matakan ne mutane ke bukata.

**"...Duk da cewa Majalisar Ɗunkin Duniya wata ƙungiyar ƙasashe ce, kundin dokokin an rubuta shi a cikin jam'i watau mu jama'ar.... Ba shakka an kafa ƙungiyar ce domin mutane, don haka dole ne ta yi wa mutane aiki duk ko'ina suke a cikin Duniya."**

Kuɓuta daga bukata: Ya na cikin manufofin taro.

A cikin rabin ƙarnin da ya wuce an sami bunƙasar tattalin arziki sosai. Amma mutane masu yawan biliyan 1.2 suke rayuwa a kan dalar Amurka ɗaya a kullum. Talauci da rashin adalci a fannin tattalin arziki tsakanin ƙasashe da kuma cikin ƙasa kanta ya saɓa wa manufar wannan ƙungiyar. Kuma hakan na ƙara sanya wasu matsalolin su munana da suka haɗa da yaƙi. Al'umar duniya yawanta na ƙaruwa ne, kuma yawan ƙaruwar jama'ar ya fi sauri a ƙasashe matalauta. Don haka kawar da talanci a duniya wani ƙalubale ne ga kowa daga cikin mu. Kuma ko da mu kasa yin wannan aikin.

***Shuwagabannin ƙasashe da gwamnatoci an umurce su da su ɗauki matakai a waɗannan wuraren:***

**Talauci.**

A shekara ta 2015 a rage yawan mutane a duniya (a yanzu da suke kashi 22 cikin ɗari) da ke da kuɗin shiga ƙasa ga dalar Amurka ɗaya duk rana.

**Ruwa**. A shekara ta 2015 a rage yawan mutanen da basu samun tsabtataccen ruwan sha a duniya (da yanzu yawansu ya kai kashi 20 cikin ɗari).

**Ilimi**. A amince da manufar nan ta rage giɓin shiga makarantar firamare da ta sakandare tsakanin jinsin maza da na mata zuwa shekara ta 2005, kuma zuwa shekara 2015 a tabbatar da cewa yara na kammala karatun makarantar firamare baki ɗaya.

**Kiwon lafiya da ciwon sida/ƙanjamau**. A hana yaduwar ciwon sida/ƙanjamau da rage yawan waɗanda suka harbu da ciwon cikin shekara ta 2015 ta:

- Daukar manufar rage harbuwa da ciwon sida a cikin mutane masu shekaru 15 zuwa 24—da kashi 25 cikin ɗari ga ƙasashen da suka fi fama da wannan cutar kafin shekara ta 2005, da kuma kashi 25 cikin ɗari a duniya baki ɗaya kafin shekara ta 2010.
- Kafa matakan kariya: A shekara ta 2005 a ƙalla kashi 90 cikin ɗari, a shekara ta 2010 a ƙalla kashi 95 cikin ɗari na matasa maza da mata dole ne su mallaki ilimin kariyar kai akan ciwon sida/ƙanjamau.
- Ga duk ƙasahen da suke fama da annobar ciwon sida/ ƙanjamau dole ne su shata manufofinsu na ƙasa cikin shekara ɗaya na wannan taron.

  Ana bukatar ƙara ƙaimi wajen bincike a fannin kiwon lafiya domin samun maganin curuta da ke damun kashi 90 cikin ɗari na mutanen duniya, kamar maganin zazzaɓin cizon sauro, tarin huka, numoniya da zawayi.

**Inganta muhallin talakawa**. A amince kuma a yi aiki da taken nan mai suna "Biranen da ba su da munanan Muhalli" wani shiri ne na haɗin gwiwa tsakanin Bankin Duniya da Majalisar Dunkin Duniya da suka ƙaddamar mai neman bunƙasa muhallin mutane miliyan 100 da ke muhallin da ake ganin ba ingantacce ba ne a shekara ta 2020.

**Gina gadar sadarwar Intanet**. A yi bitar manufofi domin kawar da duk wata matsala ta ƙaiyadewa ko farashin da zai hana mutane samun kofar sadarwar nan ta Intanet, domin tabbatar da cewa mutane basu da wata matsala wajen morewa aikace-aikacen Intanet.

***Musamman an nemi ƙasashe masu ƙarfin tattalin arziki da:***

**Hanyar kasuwanci da sauƙi.** Su riƙa barin kayan da ƙasashe da basu da ƙarfin tattalin arzikin kasa su riƙa shiga kasuwanninsu ba tare da haraji ba. Kuma ya kasance tun matakin farko su aiwatar da abin da aka amince da shi a Taron Majalisar Ɗunkin Duniya kan ƙasashe da ba su da ƙarfin tattalin arziki a watan Maris 2001, wanda ya amince da kai kayayyaki kasuwa ba tare da haraji ko ƙayyade yawan irin kayan da za'a kai.

**Sauƙaƙa bashi.** A aiwatar da shirin nan na sauƙaƙe bashi ga ƙasashe matalanta da bashi ya yi masu katutu ba tare da wani jinkiri ba. Kamar dai yadda aka amince shekarar da ta gabata, kuma a shirya soke basussukan da matalautan ƙasashe suka ciyo, sannan su kuma ƙasashen su saka wa talakawan ƙasashensu da tsare-tsaren kirki da zai rage talauci a gare su. A gaba kuma sai a ɗauki sabon mataki da zai haɗa da: sake bashin da ƙasashen da suka yi fama da yaƙe-yaƙe ko wata masifa; da zai baiwa ƙasashen daman cin gajiyar shirin karɓar bashin nan da ake kira HIPC domin matalautan ƙasashe kawai; a kuma ƙayyade abin da ƙasa zata riƙa biya daga bashin da ta ci wanda bai kai ya kawo ba daga cikin kuɗaɗen waje da ta ke samu, kuma a kafa wata ƙungiyar shiga tsakani ta masu biyan bashi.

> **"Idan har mu na son mu more wa shirin nan na 'gulobalazeshin' kuma mu kare abin da muke mora to dole ne mu koyi hanyar yin kyakkyawan mulki, dole ne kuma mu koyi hanyar yin mulkin haɗin gwiwa."**

**ODA.** A ba da taimakon cigaba ga ƙasashen da suke amfani da dukiyar ƙasar domin aiwatar da ingantattun hanyoyin rage talauci a al'umma.

**Sida/Kanjaman.** Mu yi aikin haɗin gwiwa mu da kamfanonin yin magani da duk wasu da ake ganin muhimmai ne domin samar da magani mai sauƙi don warkar da cutar nan ta ƙanjamau, kuma mu samar da hanya mai sauƙi da ƙasashe masu tasowa za su samu maganin.

**Har da Kasashen Afirka.** A yi shiri na musamman domin bukatun ƙasashen Afirka, kuma a tallafa wa 'yan Afirka a gwagwarmayar da suke yi ta ganin sun walwale matsalolin da nahiyar ta Afirka ke fama da shi.

**Kuɓuta daga tsoro:** Ra'ayin taron kan tsaro
Yaƙe-yaƙe tsakanin ƙasashe ya ragu, amma a shekaran da suka gabata yaƙe-yaken basasa ya yi sanadin mutuwar mutane miliyan 5, haka yawan mutanen da suka yi ƙaura daga gidajensu ya ninka wannan adadin da yawa. Haka nan makaman ƙare dangi na cigaba da sanya mutane cikin fargaba a kullum. Ra'ayin nan na tsaro—da da yake nufin tsare iyaka daga duk shisshigi daga waje—yanzu ya canja ya zama kariyar al'umma da mutane daga duk wani hargitsin cikin gida. Duk wata barazana ta tashin hankalin cikin gida dole ne a yi maganin ta kuma duk matakin da ta ke.
**Riga-kafi.** A shekarun da suka wuce yaƙe-yaƙe sun fi faruwa ne a ƙasashe matalauta, musamman a wuraren da ba'a yi raba daidai ba tsakanin ƙabilu ko mabiya addinai daban-daban. Hanya kyakkyawa ta riga-kafin wannan tashin hankali shi ne ta yin rabon tattalin arzikin ƙasa daidai-wa-daida, a kare haƙƙoƙin bil'Adama, haƙƙoƙin tsiraru da tsarin siyasar da duk ƙabilu za su taka rawa a cikin ta. Har-ila-yau dole ne a bar safarar makamai, kuɗi da madinai a hanyar da doka ba ta amince da shi ba.
**Kariyar masu rauni.** Dole ne a samar da hanya kyakkyawa ta aiwatar da dokar duniya akan haƙƙin bil'Adama, domin kawo ƙarshen hari ga jama'ar da ke da rauni.
**Ruɗamin da kai agaji ya shiga.** Wasu sun nuna damuwarsu cewa "taimakon jin ƙai" na iya zama wata hanya da masu mugun niya zasu leƙi asirin ƙasar da ke da 'yancin kanta—da babu mata doka da ta amince da yin hakan—ko 'yancin kai bai kamata a yi amfani da shi ba domin yin ta'addanci ga wata al'umma. Ɗaukin soje da majalisar tsaro ke bayar da umurnin a yi shi dole ne ya zama shi ne abu na ƙarshe da za'a iya yi domin tabbatar da lumana, amma a wurin da ake kisan ƙare dangi ko kisan gilla to aiki ne da ya zama bashi da makawa.
**Karfafa shirin kawo zaman lafiya.** Taron sabon ƙarnin yana kira ga a amince da shawarar da wata tawaga da Babban Sakatare ya naɗa ta bayar cewa a yi bitar duk sha'anin kawo zaman lafiya da aka yi.
**Kudurin takunkumi.** Matakan takunkumin tattali arziki wasu makafin shira ne: Domin sau da yawa suka haifar da wahalhalu ga waɗanda basu ci ba basu sha ba, kuma irin manufar da ake bukata ba'a cimmata ba. Sabin hanyoyin sanya takunkumi masu "inganci" ake son 'yan ƙungiyar su ba majalisar tsaro shawarwarin hanyoyin da ya kamata a yi su.

Kananan Makamai. Babban Sakatare na kira ga mambobin ƙungiyar da su sanya ido sosai akan hanyoyin da ƙananan makamai ke sanya hannu, ga wasu sanannun hanyoyi:

- Idan makamai zasu sanya hannu abi yadda doka ta ce.
- Karfafa hanyoyin da ƙungiyoyin nahiyoyi saka ƙirƙiro domin kwance ɗamarar yaƙi, kamar kokar nan ta shigowa, fitarwa da ƙera ƙananan makamai a Afirka ta Yamma.
- Faɗaɗa zuwa wasu sassa—musamman a ce bayan yaƙi ya ƙare a riƙa musanyan—"makamai da dukiya" shirin da ya samu karɓuwa a ƙasashe kamar su Mozambik, Panama, El Salbado da ƙasar Albaniya.

**Makaman nukiliya.** Ana son mambobin ƙungiyar su sadaukar da kansu wajen rage haɗarin makaman nukiliya da ake da su da guje wa gasar ƙera sabi, kuma su yi nazarin wata hanyar shirya taron duniya da zai shata shawarar da za'a bi domin kawar da makaman nukiliya da hadarinsu a doren ƙasa baki daya.

**Cigaba Mai Ɗorewa: Sha'anin Muhalli**

Nauyinmu ne baki ɗaya ganin cewa mun yi tanadin hanyar da al'umma da zata biyo baya ta cigaba da rayuwa a bayan ƙasa—idan muka kasa yin haka. To lallai mu na yin wasa ke nan da rayuwar yaranmu kuma za su sha wahala a gaba. Canja wannan wani irin ƙalubale ne ga ƙasashe masu arziƙi da matalanta baki ɗaya. Taron Birnin Rio da aka yi a 1992 ya samar mana da harsashen yin haka, sannan shi kuma taron Birnin Montreal akan abubuwan da ke jawo lalacewar falakin ozun wani ginshiƙin mataki ne. Amma a wasu wurare kulawarmu kaɗan ne, ya yi ƙaranci kwarai har ya makara wa sosai. Kafin Rio + 10 cikin 2002, dole ne 'yan ƙungiyar su farfaɗo da mahawarar kuma su yi shirin ɗaukar muhimman matakai a waɗannan sassan:

**Sabawa da canjin yanayi.** Rage barazanar zafin duniya na bukatar rage kashi 60 cikin ɗari na zubar sinadarin kabon da sauran sinadaran nan da ake yiwa suna da "*greenhouse gases*" ana iya bunƙasa yin hakan ne ta hanyar inganta kafafen samun makamashi, da kuma dogaro sosai a hanyoyin sabunta makamashin. Matakin farko na cimma wannan shi ne gyara manufofin taron kyoto domin ya fara aiki a cikin shekara ta 2002, don a tabbatar da an cimma manufar taron.

**Kawar da matsalolin hanyar samar da ruwa.** Rahoton na neman a amince da zangon da aka ɗiba a wajen Taron Ministocin Ruwa na Duniya: A rage zuwa rabi yawan mutanen ɗuniya da basu da hanyar samun tataccen-ruwan sha kafin shekara ta 2015. Taron har-ila-yau ya yi kira ga a zartar da wani gangami da ake wa laƙabi da "*Blue Revolution*" wanda zai ƙara samar da yawan kayan abinci daidai yawan ruwan da ake samu, da kuma bunƙasa hanyoyin kula da mashigin ruwa da madatsai.

**Kariyar ƙasa.** Kyakkyawar fatar da ake da ita ta ciyar da mutanen duniya da yawansu ya ke ƙaruwa a kullum daga filayen noma da takinsa ko albarkatunsa ke raguwa shi ne ta dogara da hanyoyin kimiyya, amma an tabbaka mahawara sosai akan irin illarsa ga mutun da ita ƙasar kan ta. Babban Ɓakatare yana son ya ƙaddamar da shiri na duniya domin ganin an walwale saɓanin da ake da shi kan hakan, domin kar masu yunwa da talakawa su yanke ƙauna.

**Kariyar gundun daji, kifi da sauran kafafe.** A duk waɗannan sassan, tsare albarkatun da ake da shi ya na muhimmanci. Don haka dole ne gwamnatoci da kamfanoni masu zaman kan su su yi haɗin gwina tare domin ƙarfafa hakan:

**"Mutanen duniya suna ce mana wai nasarorin da muka samu a da basu ishe mu ba, idan aka yi la akari da kalubalen da muke fuskanta. Dole ne nu ƙara, ƙaimi, kuma mu shi yadda ya dace."**

**Gina sabon halayyar kulawa.** Mutane da gwamnatoci dole ne su sadaukar da kansu wajen kula da kasa. Babban Sakatare ya shata wa gwamnatoci hanyoyi huɗu da ake fi so don amma wannan fatar:

- Ilmantar da jama a.
- Yin amfani da shirin nan na "*green accounting*" domin sanya muhalli cikin tattalin arziki.
- Ɗaukar matakan ƙayyadewa da• sauƙaƙa hanyoyin ciniki kamar harajin nan mai suna "*green taxes*" da dai sauran tallafi.
- Bunƙasa hanyoyin kimiyya, musamman a ce ta goyon bayan manufar nan ta taka rawa cikin hanyar bincike a sabon ƙarni, wanda ya ke mani shirin haɗin gwiwa ne na duniya domin kare lafiyar duniya.

**Sabuntar da Majalisar Ɗunkin Duniya**
Ba tare da Majalisar Ɗunkin Duniya mai ƙarfi ba za a zamo abu mai wuya sosai cimma nasarar waɗannan bukatu. Karfafa Majalisar Ɗunkin Duniya ya dogara ga gwamnatoci, musamman a ce irin sha'awarsu ta yin aiki tare wasu—kamfanoni masu zaman kan su, ƙungiyoyi masu zaman kan su da kuma kafafen hadin gwiwa—domin cimma hanyar walwale matsala da kowa ya amince da ita. Dole Majalisar Ɗunkin Duniya ta zama kanwa uwar gami wajen ƙarfafawa masu gwiwar yin aiki, kuma dole ne ta ƙirƙiro sabin hanyoyin kimiyya musamman a fannin hanyar watsa labarai.

**Babban Sakataren ya amince da ɗaukar matakai a waɗannan sassan:**

**Gane irin ƙarfinmu.** Irin ƙarfin da ta'asirin Majalisar Ɗunkin Duniya ya ke da shi ba wai ya samu ne saboda irin ƙarfin da take da shi ba a'a ya samu ne saboda irin muhimman abubuwan da ta ke wakilta, da irin rawan da ta ke takawa wajen taimakon duniya kare ɗabi'un su, da kuma dabarar da ta ke da shi na ganin duniya ta yi aiki ga abin da zai ciyar da ita gaba; haka nan da irin imanin da ta ke da shi domin ganin rayuwar mutane ta inganta. Dole mu gina wannan ƙarfin, musamman wajen tsayawa kai da fata dole a yi mulkin adalci. Har-ila-yau dole ne mu rungumi Majalisar Ɗunkin Duniya musamman domin kwaskwarima ga majalisar tsaro domin yin aiki yadda ya kamata. Dole kuma mu faɗaɗa alaƙar Majalisar Ɗunkin Duniya da al'ummar farar hula, da kamfanoni masu zaman kan su da cibiyoyi.

**Hanyar aiki bai ɗaya domin kawo canji.** Dole ne mu ƙarfafa cibiyoyin ilimin koyon karatu da na yaƙi da jahilci, domin haɗa kan cibiyoyi, farar hula da masu zaman kan su da gwamnatoci wajen cimma biyan bukata iri ɗaya.

**Hanyar wayarwa ta zamani.** Mu na iya yin amfani da sabin hanyoyin fasaha domin sanya Majalisar Ɗunkin Duniya ta yi aiki yadda ya kamata, kuma a faɗaɗa ma'amalarta da sauran duniya. Idan mu na son yi hakan dole sai mun kawar da irin al'adar nan ta hana kawo canji. Babban Sakatare na neman taimakon ƙwararru a fannin ƙere-ƙeren kayan watsa labarai domin cimma wannan manufar.

**Ciyar da sauyin ruwan sanyin gaba.** Domin cimma biyar bukatar ƙarni na 21 mu na bukatar sauyin ginshiƙan, wanda ya ke ya samu karɓuwar bai ɗaya a tsakanin 'yan ƙungiyar, sai dai kuma abin da ba'a rasa ba. Ana bukatar Babban Taron Majalisar ya yanke shawara—misali ya ƙunshi shirin nan mai "hasken rana" (*sunset provisions*) a cikin sabuwar dama kuma a fito da sabon sakamako dangane da sashen kasafi.

**Hanyar bi yanzu**

A matsayin misali na irin aikin haɗin gwiwar da Majalisar Ɗunkin Duniya ke son ta zama kanwa uwar ganinsa, Babbon Sakatare ya yi shelar matakai huɗu na ko-ta-kwana a cikin rahatonsa da ya ke son a aiwatar nan ta ke:

- Kungiyar sa kai da za'a kira Kungiyar Fasahar Sha'anin Watsa Labarai ta Majalisar Ɗunkin Duniya ("UNITeS") da zata koyar da mutane a ƙasashe masu tasowa yin amfani da kafar sadarwar Intanet da fasaharsa da irin alfanun da ya ke da shi.
- Kafar sadarwar Intanet a fannin kiwon lafiya, haɗa layin kafar sadarwar intanet a asibitin ƙasashe masu tasowa da ya kai 10,000 domin samun cikakkun bayanai na zamani da ya shafi kiwon lafiya. Asusun WebMD ne zai ɗauki ɗawainiyar wannan aikin tare da haɗin gwiwar ƙungiyar lafiya ta Duniya da Asusun Majalisar Ɗunkin Duniya da sauran ƙawayenta.
- Kungiyar kai ɗauki ga bala'i, "Nan ta ke", sune zasu samar tarho na wayar iska da na yawo a hannu ga ma'aikata aikin jin-ƙai a wuraren da bala'i ya faɗawa da wuraren da ake neman taimakon gaugawa. Wannan aikin kamfanin nan na sadarwa da ake kira Ericcson ne zai jagorance shi da haɗin gwiwar Majalisar Ɗunkin Duniya da kuma ƙungiyoyin nan na agaji da ake kira "*Red Cross*" da na "*Red Crescent*".
- Wani shirin duniya da zai ƙirƙiro ingantacciyar hanyar fuskantar rashin aiki ga matasa. Wannan ƙungiyar masana—daga shuwagabannin Bankin Duniya da ƙungiyar ƙwadago ta Duniya ce zasu jagorance shi tane da haɗin gwiwar kamfanoni masu zaman kan su da shugabannin farar hulazasu baiwa gwamnati irin abin da suka amince da shi a cikin shekara.

Muhimman Ayyuka

A ƙarshe, Babban Sakatare ya lissafa muhimman abubuwa shida da kundin dokar majalisar ya ƙarfafa da ke da ainihin muhimmanci ga wannan sabon ƙarnin: sune 'yancin kai (walwala); daidaito; da goyon baya; haƙari da juna; rashin ta'addanci ko fashin hankali; kula da mutunta sha'anin gandun daji; da rarrabawa kowa irin aikin da zai yi. Yi kira ga taron sabon ƙarnin da ya amince da shawarwari masu yawa da rahoton ya shirya, domin irin gurin da ya ke da shi na yin aiki da waɗannan abubuwan muhimmai.

**Ɗomin ƙarin bayani**

Akan kafar Intanet sai a tuntubi: http://www.un.org/millennium

Ɗaki na S-3275 Majalisar Ɗunkin Duniya
New York, NY 10017
Tel: (212) 963-5739
Fax (212) 963-0616
E-mail: millennium@un.org

Sashen wayar da kan jama'a
Ɗaki na S-955 Majalisar Ɗunkin Duniya
New York, NY 10017
Tarhon bincike: tel (212) 963-4475
Tarhon bincike na 'yanjaridu: tel (212) 963-6870
Tarhon binciken ƙungiyon da ba na gwamnati ba: tel (212) 963-8070
Fax: (212) 963-0536; e-mail: inquiries@un.org

---

United Nations

Sashen wayar da kan jama'a na Majalisar Ɗunkin Duniya ne ya ɗauki nauyin bugewa DPI/2110—mayu 2000—12M